# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da



# Samson, Mai Karfi na Allah

**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Janie Forest**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Lyn Doerksen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**

**Can shekarun baya a kasar Isra’ila, an yi wani mutum mai suna Manowa. Da shi da matansa ba su da ‘ya’ya. Wata rana sai mala’ikan UBANGIJI ya bayyana ga matan Manowa. “Za ki haifi da na musamman.” Ya ce.**



**Sai ta gaya wa maigidanta wannan labari mai ban mamaki.  Manowa ya yi addu’a, “Ya Ubangijina... zo garemu kuma.  Ka koya mana abin da za mu yi wa yaron.”**





**Mala’ikan ya gaya wa Manowa cewa ba za a taba yanka summan kai na yaron ba. Ba zai sha ruwan inabi ba. Ba kowane abinci ne zai ci ba. Allah ya riga ya zabe wannan yaron ya zama mai shari’a. Zai jagoranci Isra’ila.**





Babu shakka mutanen Allah suna bukatan taimako. Sun bar Allah a waje cikin rayuwarsu, sai abokan gabansu suka ci zalinsu, wato Filistiyawa. Amma sa'ad da suka yi addu'a, Allah ya ji su. Sai ya aika da wannan jaririn domin ya zama mutum mafi karfi a duka duniya.



“Sai macen ta haifi da namiji ta kira shi Samson: kuma yaron ya yi girma, UBANGIJI ya albarkace shi. Kuma ruhun UBANGIJI ya fara motsi a kansa.” Samson ya kasance da karfi. Wata rana ya yi fada da dan zaki da hannunsa – har ya kashe shi!



**Bayan dan lokaci, Samson ya taba zuma daga gidan kudan zuma wadanda suka yi gida a gawan jikin zakin. Sai ya kirkiro da wani kacinci kacinci: "Daga mai ci sai wani abin da za a ci ya Fito. Daga mai karfi wani mai abu zaki ya Fito."**



**Babu wani wanda ya iya gane ma’anar – amma sabuwar matar Samson, ‘yar Filisti, ta gaya wa kawayenta. Wannan ya bata wa Samson rai.**

**Samson ya kara jin haushi sa'ad da Filistiyawa suka ba da matan da zai aura wa abokinsa wanda yafi so. Sai ya shirya yadda zai rama. Amma yaya zai yi? Da farko, Samson ya kama kurenge guda 300. Sai ya daddaure wutsiyoyinsu tare, su biyu-biyu, sai ya daddaura wuta mai haske a tsakaninsu.**



Sai Samson ya sake su zuwa cikin gonakin hatsi na Filistiyawa!



Yanzu Filistiyawan suna neman su rama.  Samson ya bari an kama shi.  And daura aka kuma mika shi ga Filisitiyawa domin su kashe shi.



**Amma ruhun UBANGIJI ya sauko a kan Samson. Sai ya tsitsinke igiyoyin da aka daura shi ya dauki kashin baki na jakin da ya mutu, ya kashe abokan gaba guda dubu daya (1000).**



**Masu nema na Filistiyawa suka nemi Samson. Wata rana da daddare , sai suka yi masa kange a wata birni suka kulle kofofin birnin. Amma amson ya fita – dauke da kofofin birnin**
**a kafadarsa!**



Amma Samson ya kasa a gaban Allah.  Allah ya ba shi karfi muddin yana biyayya.  Wata rana sai ya tona atsirin karfinsa wa Delila, wata kyakyauwa ‘yar lekan atsiri na Filisiti.  Ta sa wani mutum ya aske summan kai na Samson sa’ad da yana barci.



Sa’an nan sojojin Filisti suka kai wa Samson hari a dakin kwana na Delila. Samson ya yi fada da dukan karfinsa – amma karfinsa ya riga ya bar shi. Sai abokan gabansa suka ciccire idanunsa. Ga shi makaho kuma babu karfi, Samson ya zama bawa na Filisitiyawa. Suka yi masa dariya suna wa dan hidimar Allah gori.



**Sai Filistiyawa suka yi biki. Suka yaba allahnsu-mai siffan kifi, Dagon, saboda ya ba su Samson a hannunsu. Suka sha suna farin ciki a cikin haikalin Dagon. Sa’an na suka kira Samson domin ya yi musu wasa da rawa.**



**Wani saurayi ya kawo Samson, sai ya bar shi ya jingina a ginshikai masu rike haikalin. A kan haikalin akwai Filistiyawa guda dubu uku (3000), kuma akwai wadansu**



**a cikin haikalin fiye da wadanda suke a bisa haikalin, duka suna yi masa gori da dariya.**

**Amma suman kan Samson ya fara tsira a cikin kurkuku. Yanzu sai ya yi addu'a, "Ya BANGIJI Allah, ka bani karfi sau daya a wannan karo, domin in yi ramako saboda idanuna guda biyu."**





**Ko Allah zai ba Samson karfi kuma? Samson zai iya yi abin da ba a zatta ba? I’I!**

**I’I! Cikin nishi da karfin hali, Samson ya tilasta ginshikan suka rabu. Haikalin Dagon ya rushe kurmus, ya kashe dubban mutanen Filistiyawa – duk da Samson.**

# Samson, Mai Karfi na Allah

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Alkalai 13-16**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

14

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**